# Ku ji tsoron Allah ku sallaci (sallolinku) biyar, ku azimci watanku (Ramadan) ku bada zakkar dukiyoyinku, ku bi shugabanku, zaku shiga aljannar Ubangijinku

Daga Abu Umama - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na ji manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana huduba a hajjin bankwana sai ya ce: "Ku ji tsoron Allah ku sallaci (sallolinku) biyar, ku azimci watanku (Ramadan) ku bada zakkar dukiyoyinku, ku bi shugabanku, zaku shiga aljannar Ubangijinku".
[Ingantacce ne] [Tirmizi da Ahmad sun rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi huduba a ranar Arfa, a hajjin bankwana, shekara ta goma daga hijira, an ambaceta da hakan; Domin cewa shi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya yi wa mutane bankwana a cikinta, ya umarci mutane gaba daya da su ji tsoron Ubangijinsu ta hanyar kamanta umarninSa da nisantar haninSa. Kuma su sallaci salloli biyar din da Allah - Mai girma da daukaka - Ya wajabta musu a yini da dare. Kuma Su azimci watan azimi (Ramadan). Kuma Su bada zakkar dukiyoyi ga wadanda suka cancanta kada su yi rowarta. Su kuma bi wadanda Allah Ya sanya su shgabanni akansu inba sabon Allah ba ne, wanda ya aikata wadannan abubuwan da aka ambata to ladansa shi ne shiga aljanna.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee